## Addu'a da furci domin katse dangantaka da Kalmar Shahada

*Ina katse dangantaka da dukan sadaukar da kai wanda Muhammadu ya koyas ya kuma nuna ta wurin salon rayuwarsa*

*Ina rabuwa ina kuma kin karkatattar amincewan nan dake nuna cewa Muhammadu manzon Allah ne*

*Ina nuna rashin amincewa da cewa Alkur'ani maganar Allah ce*

*Ina ki ina kuma katse dangantaka da Kalmar shahada da kuma abin da ta kunsa*

*Na ki yin* ***Fatiha****, na yi watsi da ikirarin cewa Yahudawa suna karkashin fushin Allah da kuma wai Krista sun kaucewa gaskiya*

*Ina kin magabtaka da Yahudawa, na ki yarda da cewa wai sun gurbata Littafi Mai Tsarki.*

*Na ki haddacewar Alkur'ani, kuma na ki dukan wani iko da Alkur'ani yake da shi a bisa rayuwata*

*Na ki dukan sujada ta karya da rayuwar Muhammadu take nunawa*

*Ina tsayayya da da dukan koyaswar karya game da Allah wadda Muhammadu ya koyas, da kuma cewar wai Allahn da Alkur'ani yake nunawa, shine Allah na Sama*

*Ina yin watsi da dukan sa kai da nayi a cikin Musulunci lokacin da aka haifeni, da kuma sa kan da kakanni na suka yi.*

*Ina ki, ki na musamman ga gurbin da Muhammadu ya bari, ina kin tashin hankali, tsorataswa, gaba, neman laifi, rudi, son nuna fifiko, fyade, cin zarafin mata, sata, da dukan zunuban da Muhammadu ya aikata.*

*Na ki, na kuma rabu da kumya. Ina furta cewa babu wata kayaswa ga wanda suke a cikin Kristi Yesu, kuma, Jinin Kristi yana wanke ni daga dukan kumya.*

*Na ki, kuma na rabu da dukan tsoron da Musulunci yake kawowa. Ina rokon Allah gafara domin na bari tsoron da Musulunci yake kawowa ya shiga zuciyata, na kuma zabi a cikin dukan kome, in gaskanta da Allah da kuma Uban Ubangijina Yesu Kristi.*

*Ina rokon gafara daga Allah domin wata ko kuma dukan mugunta da na aikata ta wurin bin gurbin Muhammadu a matsayin manzon Allah.*

*Na ki, kuma na raba kaina da dukan sabon dake cewa Yesu zai dawo ya tilastawa dukan mutanen duniya su bi Shari'ar da Muhammadu ya kawo.*

*Na zabi in bi Kristi, shi kadai kuma*

*Na shaida cewa Kristi shine Dan Allah wanda ya mutu a bisa giciye domin zunubaina, ya kuma tashi daga matattu domin cetona. Ina yabon Allah domin giciyen Kristi, na kuma zabi in dauki giciyena in bi shi.*

*Ina furta cewa Kristi shine Ubangijin duka. Yana mulki bisan sama da kasa. Shine Ubangijin rayuwata. Na yarda cewa zai komo domin ya yiwa masu rai da matattu shari'a. Na mannewa Kristi na kuma shaida cewa babu wani suna a sama ko a kasa wanda za'a sami ccto a cikinsa sai sunan Kristi.*

*Ina gayyata Allah Ubaya bani sabuwar zuciya, zuciya ta Kristi, domin ta jagorance ni cikin dukan abin da nake aikatawa ko nake fadi.*

*Nayi watsi da dukan sujada da ba ta gaskiya ba, na kuma mika jikina domin yin sujada ga Allah mai rai, Allah Uba, Allah Da da Allah Ruhu Mai Tsarki.*